# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Wani Shugaban Haikali ya Ziyarci Yesu


**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Byron Unger; Lazarus
Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: M. Maillot; Sarah S.**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**



**Wanda ya Wallafa: Bible for Children
www.M1914.org**



**©2024 Bible for Children, Inc.**

**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan
har ba zaku sayar da shi.**




**Sa’ad da Yesu ya tafi Haikali wata rana, sai ya sadu da mutanen da suna ayyukan da ba ya daukaka Gidan Allah. Suna sayar dabbobi suna canja kudade a cikin Haikalin!**




Sai ya gyara bulalla da igiyoyi, Yesu ya kokkore masu kasuwanci daga Haikali. “Ku kawar da wadannan abubwan,” ya umarta. “Kada ku mai da Gidan Ubana wurin kasuwanci.” Yesu yana kaunar Gidan Ubansa.
3
Shugabanin suka bukaci alama wanda zai nuna cewa Yesu yana da ‘yanci ya share Haikalin. “Ku rushe wannan Haikalin ni kuma zan sake gina shi a cikin kwana uku,” Yesu ya amsa. Ba zai iya faru ba! An dauki shekaru arbain da shida kafin a gama gina wannan Haikalin.
4
Amma Yesu ya yi magana game da jikinsa ne. Kamar Haikali, Jikinsa wurin zaman Allah ne. Ko da yake Yesu zai mutu a kan giciye, ya sani cewa Allah zai tashe shi daga mutuwa a rana ta uku.
5
Da daddare, daya daga shugabanin Haikalin ya ziyarci Yesu. Ya sani cewa Allah ne ya aike shi ta wurin ayyukan al’ajibin da Yesu ke yi. Nikodemus ya zo wurin Yesu domin ya karu game da sanin Allah.
6
Yesu ya fada wa Nikodemus cewa dole mutane su sake haifuwa kafin su shiga Mulkin Allah. Nikodemus bai gane ba. Yaya za a ce mutum da ya riga ya yi girma zai iya zama jariri kuma? Ban da haka ma, shi mai bi ne. Wannan bai isa ba?
7
“Abin da ruhu ya haifa ruhu ne,” Yesu ya bayana. “Ruhun Allah kamar iska ne. Mutane ba sa gani ko gane yadda iska yake. Suna ganin abin da iska ke yi ne kawai.”
8


Yesu ya tunashe Nikodemus game da gunguni na ‘ya’yan Isra’ila ga Musa tun a da. “Ba mu da abinci, babu ruwa, kuma ba ma son burodin da Allah yake ba mu,” sun yi kuka.
9


Zunuban mutanen yasa Allah fushi. Sai ya aika da mugayen macizai a tsakiyar mutanen. Macizan suka sassare mutanen. Da yawa sun mutu.
10


“Mun yi zunubi. Ka yi addu’a domin UBANGIJI ya kawar da macizan,” mutanen suka roka. Sai Musa ya roka a madadinsu. Amma Allah bai kawar da macizan ba.
11


Allah ya gaya wa Musa ya yi wani maciji mai ban tsoro sa’an nan ya kafa shi a inda kowa zai iya gani. “Duk wanda macijin ya sare shi zai rayu idan ya kalli macijin da aka kafa,” Allah ya yi alkawari. Musa ya yi maciji na tagula kuma duka wadanda suka kalli shi sun warke.
12


Yesu ya fada wa Nikodemus cewa dole ne a daga Dan mutum a sama kamar yadda aka daga macijin tagula. Yesu ya yi maganan giciye inda zai mutu saboda masu zunubi ne.
13


Yesu ya ce, “Allah ya kaunace duniya sosai har ya ba da Dansa makadaici, don duk wanda ya ba da gaskiya a gare shi kada ya halaka amma ya sami rai na har abada.”
14




15

Watakila Nikodemus bai zama almajirin Yesu a daren nan ba. Amma shekaru nan gaba, Nicodemus ya nuna cewa yana kauna yana ba da gaskiya a kan Yesu ta wurin taimakon da ya yi na bizne Dan Allah wanda aka giciye.



16

Bayan wannan, Yesu da almajiransa suka fara tafiya zuwa Arewa. Ana bukata wadansu su ji labarin Mulkin Allah, su kuma sami zarafin ba da gaskiya ga Yesu na Nazaret, Dan Allah.




17

Wani Shugaban Haikali ya Ziyarci Yesu

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Yohanna 2-3, Kiddaya 21

"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130

18




41

60

19

Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin
Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.

Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.

Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:
Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.

Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16

20